Ka tafi zuwa gareshi ka ce masa: Lallai kai ba ka cikin 'yan wuta, sai dai kana daga cikin 'yan aljanna

Daga Anas Ɗan Malik Allah Ya yarda da shi Lallai Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya nemiSabitu ɗan Ƙais (domin bai ganshi ba) sai wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah, ni zan samo maka labarinsa, sai ya zo masa sai ya same shi a zaune a gidansa ya sunkuyar da kansa, sai ya ce: Meke damunka? sai ya ce: Sharri, ya kasance yana ɗaga sautinsa sama da sautin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, to, haƙiƙa aikinsa ya ɓaci, kuma shi yana daga 'yan wuta. Sai mutumin ya zo sai ya ba shi labarin cewa kaza da kaza, sai ya dawo a karo na ƙarshe da babban albishir, sai ya ce: "Ka tafi zuwa gareshi ka ce masa: Lallai kai ba ka cikin 'yan wuta, sai dai kana daga cikin 'yan aljanna".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya rasa Sabitu Dan Ƙais - Allah Ya yarda da shi - ya yi tambaya game da shi (ya yi cigiyarsa), sai wani mutum ya ce: Ni zan samo maka labarinsa, da dalilin fakuwarsa, sai ya tafi wurinsa sai ya same shi yana cikin baƙin ciki yana mai sunkuyar da kansa a gidansa, sai ya tambaye shi : Meke damunka? sai Sabitu ya ba shi labarin abin da ke tare da shi na sharri; domin cewa ya kasance yana ɗaga sautinsa sama da sautin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, kuma haƙiƙa Allah Ya yi alkawarin narko daga aikata hakan da ɓacin aikinsa, kuma cewa shi yana daga 'yan wuta! Sai mutumin ya dawo zuwa ga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya sanar da shi da hakan, sai Annabi - tsaira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya umarce shi ya koma wa Sabitu ɗan Ƙais ya yi masa albishir da cewa shi ba ya daga 'yan wuta, sai dai yana daga 'yan aljanna, domin cewa ya kasance mai babbar murya ne a halitta, domin shi ya kasance mai huɗubar Manzon Allah ne - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -. kuma mai yi wa mutanen Madina huɗuba.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/65073